An kirawo shi ne da Alkidr saboda ya zauna akan wata Qasa Busashiya fara, sai kawai ta riqa motsi a bayansa ta koma koriya

An rawaito daga Abu Huraira -Allah ya yarda da shi daga Annabi SAW ya ce: "An kirawo shi ne da Alkidr saboda ya zauna akan wata Qasa Busashiya fara, sai kawai ta riqa motsi a bayansa ta koma koriya"

[Ingantacce ne] [Buhari ne ya rawaito shi]

Annabi yana bada labarin cewa An kirawo shi ne da Alkidr saboda ya zauna akan wata Qasa Busashiya fara, sai kawai ta riqa motsi a bayansa ta koma koriya, saboda abunda ya futo a cikinta na ciyayi da koren ganye, Maganarsa a zo cikin Qur'ani a cikin Qissar Annabi Musa a Suratu Alkahf, kuma Malamai sunyi savani kan cewa wai shi Annabi ne ko kuma Waliyyi ne bawan Allah, zance mafi inganci Annabi ne

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/10995